# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Yesu ya Kwantar da Teku mai Hauka



Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Janie Forest
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2024 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.





Yesu da almajiransa suna a cikin kwalle-kwalle sai wani babban hadari ya taso. Yana dukan igiyoyin ruwan Tekun Galili har yana hauka. Irin wannan hadari zai iya sa jirgin ruwa ya nutse ya shiga karkashin tekun.

Hadarin ya ba wa almajiran tsoro mai tsanani. Rakuman ruwa suka rufe kwale-kwalen, ruwa ya shiga ko'ina. Amma Yesu yana zurfin barci a matashin kai, barci a cikin hadarin. Sai almajiran suka tashe shi suna kuka, "Maigida, Maigida, muna cikin halaka."



3

"Don me kuke jin tsoro, ya ku masu kankantan bangaskiya?" Yesu ya tambaye almajiransa. Sai Yesu ya umarci iskan ya dena huruwa... Kuma… Yesu ya umarci rakuman ruwa su kwanta su kuma bar haukan…



4

SAI ISKAN YA TSAYA CIK… TEKUN YA KWANTA SHIRU YA KUMA BAR HAUKAN. Almajiran suka yi mamaki, suna cewa, "Wane ne wannan, wanda har ma iska da teku suna yi masa biyayya!"



5

Bayan dan lokaci, Yesu ya kasance da ayyuka masu yawa a ranar. Mutane fiye da dubu biyar ne 5000 suka bi shi zuwa wurin da ba kowa. Ta wurin ikon Allah, Yesu ya ciyar da dumbun taron jama'a da dan abincin rana na wani karamin yaro. Yanzu yamma ya yi. Yesu ya sa kowa ya tafi.



6

Har ma da almajiran, su ma suka tafi. Yesu ya sa suka shiga su sha gabansa zuwa wancan gefen Tekun Galili.



7

Bayan da ya sa kowa ya tafi, Yesu ya hau zuwa tudu shi kadai domin yayi addu'a. Bayan da yamma ya yi, ya kasance shi kadai a wurin.



8



A waje wurin tafjin ruwa, sai wani iska mai karfi ya kama su. Gugguwar iskan ya hana su ketare ruwan, ko da yake sun yi ta kokari na sa'o'I masu yawa. Almajiran ba su sani ba, ashe akwai abin ban mamkin da ke jiransu!

9



Tsakani karfe uku da karfe shida na safe, a tsakiyar wannan teku mai gugguwan iska, sai almajiran suka ga wani abu wanda ya ba su tsoro sosai. "Fatalwa ne!" suka yi ihu. Amma Yesu ne, Ubangijinsu da Maigidansu, yana zuwa wurinsu, YANA TAFIYA A KAN RUWA.

10

"Ku kasance cikin farin ciki!" Yesu ya kira su. "Ni ne; kada ku ji tsoro." Bitrus ya amsa, "Ubangiji, idan kai ne, sai ka umarce ni in zo, gareka a kan ruwan." Sai Yesu ya ce, "Zo." Cikin karfin zuciya, Bitrus ya cire kafa daga jirgin ruwan sai ya saka a kan ruwan, ya fara tafiya zuwa wurin Yesu.



11



Amma sa'd da ya gan iskar na karuwa da karfi, Bitrus ya ji tsoro sai ya fara nutsewa. Ya yi kuka, Ubangiji, "ka cece ni!"

12



Nan da nan, Yesu ya mika hannunsa ya kama Bitrus. "Ya kai mai karamin bangaskiya, domin mene ne ka yi shakka?" Ya tambaye shi. Kuma sa'ad da Bitrus da Ubangiji suka koma cikin jirgin ruwan, sai iskar ta daina.

13



Sa'an nan wadanda suke a cikin jirgin ruwan suka zo suka yi wa Yesu sujada, suna cewa, "Da gaske, Kai ne Dan Allah."

14

**Yesu ya Kwantar da Teku mai Hauka**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Matiyu 8, Matiyu 14,**
**Markus 4, Luka 8**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**






48 60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**